# AREWA24 Ta Kaddamar Da Sabon Mobile App Na Hausa A Android Da iOS

**17 ga Maris, 2016** – AREWA24, gidan talabijin da ke kan tauraron Dan-Adam na farko a Hausa mai yada shirye-shirye awa ashirin da hudu kyauta da 'yan Arewacin Najeriya su ke yi don Arewacin Najeriya, ta samu nasanar kaddamar da App dinta na wayar hannu da za a iya samu a Google Play Store da kuma Apple App Store. App na AREWA24 karin wata hanya ce ta fadada samun tashar AREWA24 da zai bawa 'yan kallo da masoya damar kallon shirye-shiryen AREWA24 a lokacin da suke so a wayoyinsu na hannu. Sabon App din zai kunshi shirye-shiryen AREWA24 ne na kashin kanta, da suka kunshi al'amuran rayuwa na yau da kullum, al'adu da al'amuran da su ka shafi 'yan Arewacin Najeriya. Yanzu, masu magana da harshen Hausa a duk fadin Afirka, gabas ta tsakiya da kuma sauran bangarorin duniya, za su samu sanannun ingantattun shirye-shiryen da su ka shafi ko wanne fanni da ma'aikatan AREWA24 su ka yi a Kano.




Hotunan shafi daga AREWA24 app (daga hagu zuwa dama):
1) Shafin jerin shirye-shirye; 2) Shafin kafofin sada zumunta; 3) Shafin shirye-shirye masu zuwa.

App na AREWA24 ya bawa masu amfani a duk fadin duniya damar shiga tsarin shirye-shiryenmu kai-tsaye da sukahada da::

- Kallon shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta lokacin da mutane ke so;
- Kallon shirin Dadin Kowa, wasan kwaikwayon AREWA24 da ya lashe gasa, kafin lokacin nuna shi;
- Adana shirin da kuka fi so domin saukin nemowa;
- Duba tsarin shirye-shirye na kullum da kuma na sati;
- Saduwa da tashar kai-tsaye da kuma sauran masu kallo ta hanyar kafofin sada zumunta;

- Samun sako yayin da aka dora wani sabon abu da ake bukata;
- Ku turo sako ta hanyar SMS da kuma ta hanyar amsa sako ta hanyar waya (IVR)

Duk da cewa muna da kyautata zaton mafi yawan sababbin masu kallo za su kasance 'Yan Najeriya, Kididdiga daga kafafen sada zumunta na AREWA24 sun nuna cewa akwai wasu da dama daga wasu bangarorin na Afirka ta Yamma, Gabas ta Tsakiya da sauran bangarorin duniya..

A cewar Rakiya Usman, manajar shirye-shirye ta AREWA24, "Wannan sabon App zai bamu damar kaiwa ga masu amfani da wayar hannu a Najeriya da duk fadin duniya da shirye-shiryenmu na kashin kanmu masu nishadantarwa a harshen Hausa." Kuma ta kara da cewa, "Mun dukufa wajen kare kambun mu na wadanda su ka fi kowa samar da shirye-shirye ingantattu, kayatattu, masu ilimantarwa da kuma nishadantarwa a harshen Hausa, sannan kuma mu tsaya da kafarmu a kan sabuwar fasahar sadar da shirye-shirye ta wayar hannu."

Wannan App din fitaccen kamfanin da ya lashe gasa ne da ke San Fracisco, ArcTouch ya gina shi kuma ya tsara shi. A cewar daya daga cikin wadanda su ka kirkiri kamfanin ArcTouch, Adam Fingerman, "Muna alfahari da muka taimakawa Arewa24 ta kirkiro sabuwar hanyar cudanya da masu kallonta. A lokacin da muke aiki tare da ma'aikatan Arewa24, babban burinmu shine mu tsara App din da zai bawa masu amfani da shi damar da za su yi amfani ta hanyoyi da dama cikin sauki don su kalli shirin da suka fi so a lokacin da suke so."

**GAME DA AREWA24 :**AREWA24 (arewa24.com) GAME DA AREWA24: AREWA24 (arewa24.com) gidan talabijin din Arewacin Najeriya ne na farko a tauraron Dan-Adam mai yada shirye-shiryensa awa ashirin da hudu kyauta, wanda ke gabatar da shirye-shiryensa a kan rayuwar Arewacin Najeriya, al'adu, matasa, kasuwanci da nishadantar da iyali. AREWA24 ta dukufa wajen habakawa da kuma cike gibin da masu magana da harshen Hausa su ka rasa na shirye-shiryen Hausa a duk fadin duniya, wadanda da yawansu su kan kama tashar AREWA24 ta hanyar yanar gizo domin ganin al'adarsu da kuma ta sauran mutanen duniya.

Ana dora shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta ko wane sati a youtube.com/AREWA24channel, kuma tashar tana karuwa da masu kallonta ko da yaushe a AREWA24.com, facebook.com/AREWA24, Instagram.com/AREWA24channel, da twitter.com/AREWA24channel. AREWA24 ta na kan EUTELSAT 16A, horizontal polarization, frequency 10804, symbol rate 30000 da kuma tauraron Dan-Adam na ACTV. Abokan huldar AREWA24 sun hada da Jordan Media City, Eutelsat da Globecast. Ana rarraba shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta a duk fadin Arewacin Najeriya tare da hadin gwiwar hukumar talabijin ta Najeriya (NTA). Tashoshin da suka fara gudanar da wannan hadakar ta NTA-AREWA24 sun hada da NTA-Abuja, NTA-Bauchi, NTA-Kaduna, NTA-Kano, NTA-Maiduguri da NTA-Sokoto, kuma zamu ci gaba da kutsawa cikin sauran tashoshin NTA a Arewacin Najeriya gabadayan wannan shekarar.

###